GEMS4

Mai sari/ mai kasawa



# Gina Gidan Tattara Kayan Lambu

## Tsayayyun Ka'idojin Gudanarwa

GEMS4

Mai sari/ mai kasawa

UKaid

From the British people

## Menene gidan tattara amfani?

## Abun da ya kunsa

**Gidan tattara amfani**

Menene gidan tattara 2

**Gina gidan tattara amfani**

Wuri 2

Ginin 3

Tsara gidan tattara amfani 5

Gudanarwa 7

Samar da ma'aikatan giidan tattara amfani 10

**Sauran bukatu**

Tsafta da kwashe shara 11

Kiwon lafiya da kariya 12

Kudin da za ake bukata 12

Gidan tattara amfani shi ne ginannan gida inda ake tsaftace kayan lambu da aka cire, ake wawware su, ake tantance girmansu kana ake shirya su a mazubi domin a siyar a kasuwannin kayan marmari bayan an rarraba su. Dole ne a samu tsarin hada-hada da za a tafiyar kana a kula da shi a cikin gidan tattara amfanin.

Ana iya tsara gidan tattara amfani da nufin samar da amfani ga manyan cibiyoyin cinikayya, irinsu manyan shagunan cinki inda ake baiwa darajar amfani fifiko.

Gidajen tattara amfani sun karkasu, kama daga kananan gine-gine da aka kewaye zuwa manya da aka sanya mu su kayan alatu na zamani. Sun kuma karkasu gwargwadon irin amfanin ko yawan hada-hada, bakidaya sannan da tanadin fadada shi nan gaba.

## WURI

ka'idojin da za a lura da su yayin tantance wurin da za a gina a matsayin gidan tattara amfanin gona.

a. **Kusaci da inda ake noma amfani ko abokan hulda:** Wannan na da muhimmanci yayin hada-hada mai yawa a wuri mai fadin gaske; yana saukaka hanyar samun masu noma amfani akai-akai, da masu siya da kuma masu sarrafawa. Za kuma a samu saukin zuwa gonakin, musamman ta titunan mota. A wasu lokutan, musamman inda ya ke da wuya a kusa a samu kyayyakin da ake bukata wajen tsaftace kayan lambu da kyautata darajar su. Zai fi dacewa a gina gidan tattara amfani a muhallin (wato kusa da kasuwar mabukata)
b. **Wurin Ginin-** Ya kamata wurin da za a gina gidan tattara amfani ya zama mai yalwa ta yadda za a samu sukunin fadada shi nan gaba. Wurin da aka zaba ya kasance yana da kariya kuma mai fadi sosai ta yadda ababan hawa da manyan motocin daukar kayan za su iya juyawa. Dole ne a kare wurin daga kura da iska da zaizayar kasa da kuma ambaliya.
c. **Ma'aikata-** Dole a samar da isassun ma'aikata a yankin da ake tafi gidan tattara amfani.
d. **Kayan aiki da aiyukan-** Dole ne a iya samar da ayyukan cikin sauki; wannan ya kunshi ababe irinsu tsaftataccen ruwa da lantarki da na'urorin sadarwa domin tuntubar masu siye da siyarwa da tituna da layin dogo domin saukaka safarar amfani da kuma damar samun kayayyakin da za a yi amfani da su a gidan.

## GINE-GINE NA ZAHIRI

### Dabe

a. Dabe na kankare domin saukaka hada-hadar mutane da amfani.
b. Dabe mai inganci da zai sanya a samu saukin kwararar ruwa da wanke shi bayan an tattara shi, ana nufin dole ne magudanar ruwan ta zama mai inganci.
c. A duk inda daben ya hadu da bango, ba a bukatar a samu kusurwa; haka ne zai hana ruwa kwanciya kana zai sanya a samu saukin sharewa.

### Jikin bango

a. Dole ne jikin bangon ya yi sumul kuma a yi mishi fenti mai haske mai nagarta (mai hana yaduwar gamsa-kuka)
b. Mai saukin yayin gogewa wanda zai hana yaduwar gamsa kuka.
c. Dole ne a yiwa bangon waje fenti ko kuma filasta domin kare nason ruwa a bangwayen.

### Rufi

a. Dole ne ginin ya samu cikakkiyar kariya ta sama daga hasken rana.
b. Nau'in rufin dakin: kwano ko kuma ko wane irin abun rufi da ya dace wanda baya rike zafi.
c. Dole ne kayan rufin su zama masu tsafta, ba matattuba kana wadanda ba za su karareye ba nan gaba.
d. Za a iya yin amfani da abun rufi marasa duhu domin samar da haske a cikin gidan tattara amfani. Sai dai kuma za a iya yin amfani da su ne idan akwai ishasshiyar iska, ganin ababan rufi marasa duhu na iya karawa ginin zafi.
e. Dole ne a yi rufin ta yadda ruwa zai dinga kwaranyewa cikin sauki.

### Kewayawar iska

a. Dole ne a yi ginin domin ya samar da ishasshiyar iska yayin da ya ke samar da kariya.
b. Kimanin kaso 25 cikin dari na jikin katangun su zama a bude don a samar da kewayawar iska yadda ya kamata.
c. Dole ne a tantance kafafen shigar iskar domin kare shigar kwari, tsuntsaye, tsutsotsi da sauran dabbobi ko kwari masu hadari ko kuma duk wani abu da ka iya gurbata amfani. Kalar abun rufi da aka amince shi ne wanda zai hana kwari shiga.

**Hoto na 1:** Mashigar iskar ta kai kaso 25 cikin dari na bangon ginin gidan.



## Haske da lantarki

a. Dole ne a sanya wa ginin lantarki kuma a samar da ishasshen haske domin a samu sukunin wankewa da wawwarewa da kuma tattarawa.
b. Zabin hasken da zai kasance a cikin ginin tattara amfanin ya kusa kaiwa ga hasken rana gwargwadon iko. Hakan zai tabbatar da fayyace launi cikin sauki yayin karkasa amfani bisa kima, kana ba za a samu gauraya kashe-kashen shi ba.
c. Launin tsanwar haske na kawo kwari sannan ana iya ajiyewa a can gefe guda domin a nesanta kwari daga ginin gwargwadon iko.
d. Za a lullube kwayayen fitilu domin a kare gurbata amfani daga buraguzan kwan fitalar idan sun fashe.

## Kofofi

a. Dole ne daukancin kofofin su kasance masu kullewa da kansu.
b. Dole ne daukacin kofofin su kasance masu fadi sosai ta yadda za a dinga iya wucewa da manyan kwanduna da kuma madaukan kwandunan.

## Magudanan ruwa

a. Dole ne a tsara magudanan ruwa ta yadda ruwa zai dinga tafiya, haka ma ruwan da aka yi amfani da shi wajen sarrafa amfani ko wanke-wanke ba tare da haifar da barazanar ga muhallin ba.
b. An bayar da shawarar yin budaddiyar magudanar ruwa domin saukaka wanke-wanke sannan a samu damar fitar da gurbatattun amfani daga gidan tattara amfani.
c. Dole a tsara magudanar ruwa yadda za ta kare shigar kwari ko dabbobi masu hadari.

**Hoto na 2:** Ya kyautu a rufe magudanar ruwa domin kare shigar muggan dabbobi da sauran kwari.



### Makewayi da tsaftar jiki

a. Dole kofofin makewayi ba za su fuskanci dandamalin sarrafa amfani amfani ba kai tsaye idan an bude su.
b. A mafi yawancin lamurra, dole a samar da makewayin a wani ginin ba na tattara amfani ba.
c. Ya kyautu a samar da wuraran wanke hannu da sabulu da sinadarin tsaftace hannu da tsumman goge hannu da kuma na'urar busar da hannu.

## TSARIN GIDAN TATTARA AMFANI

Kama daga saukewa zuwa lodawa, za a dinga shigo da sabon danyen amfani ta fuska guda tare da tabbataccen muhallin gudanarwa tasararre. Dole a samu tsayayyen muhallin karba da warewa da wankewa da karkasawa da zubawa a mazubi da kuma ajiye sabon danyen amfani da wadanda ba a sarrafa ba da ma wadanda aka sarrafa. Dole a fuska guda da ake shigo da amfanin ta dore ba tare da la'akari da yawan hanyoyin da ake bi a gidan ba.

a. Dole ne tsarin ya kasance wanda zai bayar da damar zirga-zirgar mutane da amfanin ba tare da tarnaki ba a daukacin gidan zuba amfanin a mazubi.
b. A samu wuri na daban da za a dinga karba da rubuta bayanai da wawwarewa da wankewa da ajiyewa da tattarawa da kuma wuraran yin lodi. Dole a samu ishasshen filin ajiye kayan aiki da sinadarai da gurin ajiye amfanin da aka kawo wuri guda.
c. Dole ne a ajiye daukacin takardun hulda game da hada-hadar a wurin ofisoshin gidan tattara amfanin da aka ware.
d. Dole a ajiye sinadarai a gefe guda a killatacce, da aka takaita shiga, mai yalwar kewayawar iska.
e. Dole ne a samar da wurin canja kaya na ma'aikata domin baiwa kai kariya gabanin hawa daben sarrafawa.

**Hoto na 3:** Wurin tattara amfani mai nuna hanya guda ta zirga-zirga.

---------------------------------------------------------------------------------------------------------------------
-------------------------

| | | |
|---|---|---|
| Ofishi | wurin karbar kaya | wurin adana amfanin da aka karba |

-------------------------------------------------------------------------------------

| | | |
|---|---|---|
| wawwarewa | wankewa | karkasawa |

-------------------------------------------------------------------------------------

| | | |
|---|---|---|
| kwandunan roba da | Zubawa a mazubi | Adanawa a kwalaye |

-------------------------------------------------------------------------------------

| | | |
|---|---|---|
| Wurin ajiya mai sanyi | wurin lodi | ajiye amfanin da aka sarrafa |

-------------------------------------------------------------------------------------

## GUDANARWA

### Kayan aiki

Muhimman kayayyakin aikin da ake amfani da su a gidan tattara amfani sun hada da:

a. **Teburin wawwarewa:** Wanda aka lullube shi da kwanon karfen da baya tsatsa ko robar karkasa amfani ko kuma sinadari.
b. **Tankunan wanke-wanke:** Masu tsawon da za su kai centi mita 75 wanda aka yi da karfen da baya tsatsa ko robar karkasa amfani.
c. **Manyan tebura ko mazubai:** Teburin ya zama an yi shi da ragar roba domin fitar ruwa gabanin a zuba a mazubi. Manyan mazuban su zama na karfen da baya tsatsa ko kuma roba sannan dole ne a sada shi da magudanar ruwa domin a zubar da ruwan aikin da ya gurbata.
d. **Teburin karkasawa:** Wadannan zasu kasance an yi su ne da karfen da baya yin tsatsa ko kuma roba. Idan anyi da katako ne to dole ne a lullube saman shi da malullubin roba, misali sinadarin karkasa abinci.
e. **Ma'auni:** Za a yi amfani da wannan ne wajen awon amfanin da aka kawo ko kuma wandanda aka kammala sarrafawa.
f. **Mazuban katako ko na roba:** Domin ajiye amfanin da aka kawo ko wadanda aka sarrafa sannan kayan tattarawar wato; kwalaye ko kuma kwandunan roba.
g. **Keken daukar Kaya a Mazubai:** Wannan na nufin na'ura ko keken daukar amfani mai nauyi ko maras nauyi da aka zuba a mazubi da akan yi zirga-zirga da shi a cikin gidan da ake tattara amfani.
h. **Manyan mazubai (na karfe marasa tsatsa ko na roba):** Za a yi amfani da wadannan ne domin ajiye sabon danyen amfani na wucin gadi gabanin a zuba a mazubi.
i. **Kwandunan roba da za a dawo da su ko kwandunan kwalaye: Ana amfani da mazubin roba a dauki amfanin gona zuwa wajen sarrafawa ko sayarwa. Sannan ana amfani da kwalaye wajen zuba amfanin goda wanda ake da niyar sayarwa da wuri a zuwa kasuwanni ga masu saye.**
j. **Kayan zama:** Kujerun ma'aikata da kayan zama na ofis na katako.
k. **Kayan wanke-wanke:** Wadannan sun hada da tsummunan tsane ruwa da tsintsiya da burushi.
l. **Kayan kare kai:** Wadannan sun hada da abun kare fuska (ba na kare kura ba), hulunan rufe kai, rigunan baiwa kai kariya, safunan hannu na roba da takalman roba ko kuma takalmi sau ciki. Doguwar riga ta kariya na iya zama dole a wasu lokutan.

Idan aka bukaci yin amfani da injina, ana iya yin amfani da abun daukar kaya na turawa. An yi shawarar ayi amfani da wadannan a hada-hada mai tarin yawa.

## Gudanawar gidan tattara amfani

### Karba.

a. Dole ne a baiwa wurin karbar kayan amfani kariya daga yanayin da ake ciki.
b. Guri ne mai kazanta dan haka dole a ware shi daga wurin da ake yin lodi inda za a adana amfanin da aka sarrafa.
c. Dole a samar da kayayyaki a gidan tattara amfani na sanya idanu, aunawa da rubutun alama da kuma rubuta bayanan kwanan wata da inda aka kawo amfanin.
d. Ya kyautu wurin karbar amfanin ya kasance mai fadin gaske domin a samu sukunin sarrafa amfani mai yawa.
e. Ya kyautu dukkan kayan amfanin da aka karba a rubuta bayanan su ta hanyar
    i. Sunan mai shi
    ii. Nauyi
    iii. Inda aka samo amfanin (don saukaka bibiya idan an samu barkewar cuta sanadiyyar yin amfani da shi)
    iv. Kalar amfanin
    v. Yawan mazubai
    vi. Kwanan watan da aka shiga da shi gidan tattara amfani.

### Wawwarewa


a. Wawwarewa na nufin ware amfanin da ba za a karba ba da kuma wadanda ba za su karbu a kasuwa ba.
b. Za a ajiye wadanda ba a karba ba a gefe domin a kawar ta hanyar siyar wa ga masu sarrafawa ko kuma a watsar da su nan take.
c. Za a mika amfanin da suka cancanci kaiwa kasuwa wajen wankewa.
d. An amince cewa teburin wawwarewa kashi na biyu da za a tabbatar da nagartar amfani bisa taburin wawwarewa na farko an samar da shi domin a tabbatar ba amfanin da aka ki karba da ya samu shigewa.
e. Ana iya sake tantance amfanin da aka ki karba domin a tsince dukkan amfanin da ka iya samun shiga a kasuwa gabanin a zubar.

**Hoto na 4:** Jadawali mai nuna yadda ake wawware tumaturi

Mai kyau- Zai tafi wajen wanki

Maras kyau- Ana iya shanyawa ko a yi lemo

Rubabbe- Za a zubar a matsayin maras kyau




Mai kyau maras kyau Rubabbe

## Wankewa

a. Dole ne a wanke wadannan kayan amfanin, irin su kayan marmari masu yawa da ganyayyaki da ruwa mai kyau domin a cire hakkokin da ba a bukata a jikinsu (idan ya zama dole).
b. Yin amfani da sinadarin wanki (sodium hypoclorite) gwargwadon mililita 25 kwatankwacin lita 20 na ruwa za a kara a ruwan wankin a matsayin sinadarin kashe kwayoyin cuta.
c. Danyun amfani irin su tumatur za su shafe a kalla mintuna 2 a cikin ruwan.
d. Za a bar amfani ya bushe bayan an wanke.
e. Tare da amfanin da ba kayan marmari ko kayan lambu ba wadanda yanayin barazanar gurbata ta ke da yawa sosai, ya fi dacewa a goge da kyalle mai danshi.
f. Dole a share ruwan da aka yi amfani da shi cikin gaggawa.

### Karkasawa

a. Za a karkasa amfani ne gwargwadon nunar shi.
b. Ga tumaturi, misali, za a ware koren tumatur daga nunannu jajaye. Za kuma a karkasa wadannan a manya da kanana domin farashi mai gwabi a kasuwanni.

### Zubawa a mazubi

a. Za a zuba danyun amfani a mazubin roba da leda ko kuma kwali gwargwadon bukatar mai shi.
b. Dole ne a wanke dukkan kwandunan roba da sinadarin kashe kwayoyin cuta na ruwa kana a busar da su kafin a ajiye.
c. Dole a rubuta cikakkiyar alama a daukacin mazuban da aka zuba amfani domin sheda a wurin ajiya.
d. Dole a kawar da mazuban da suka lalace.

### Rikewa ko Ajiye

a. Ga amfani mai saurin narkewa, an bada zabin ajiyewa cikin kankara.
b. Za a ajiye sauran amfani a inda iska take zagayawa.
c. Dole ne a ajiye amfani a budaddun mazuban katako.

## MA'AIKATAN GIDAN TATTATARA AMFANI

Gidan tattara amfani na bukatar ma'aikata domin aiwatar da wadannan ayyukan:

a. Saukewa da lodawa
b. Karba
c. Wawwarewa
d. Wankewa
e. Karkasawa
f. Zubawa a mazubi
g. Masu sanya idanu (a ko wane bangaren aikin)
h. Shugaban gidan tattarawar
i. Masu shara
j. Masu gadi

Yawan ma'aikatan a ko wane bangaren aiki ya dogara ga girma da hada-hadar gidan tattara amfanin.

## SAURAN BUKATU

### Tsaftar muhalli da zubar da shara

#### Tsaftace muhallin

a. Za a share daukacin yankin daben, a goge kana a sanya maganin kashe kwayoyin cuta a karshen ko wane canjin aiki.
b. Dole ne a goge dukkan layuyyukan tattarawa da wurin yin amfani da kayan aikin, a wanke sannan a wanke da maganin kashe kwayoyin cuta irin su sinadarin 200 p.p.m. na sodiumhypochlorite (sinadarin hasken wanki gwargwadon ml 25 a kowace litar ruwa 20) kafin a fara hada-hadar kayan marmari bayan ko wane zangon canjin aiki
c. Za a tattaro daukacin rubabbun kayan marmari, kwanduna da sauran tarkace daga wurare daban-daban kana a zuba su a kwandon shara ai murfi wanda zai kasance a nesa da gidan tattara amfanin da za a fitar da shi a ko wace rana. Ba za a bar kazantar mutane kusa da gidan tattara amfani ya kwana ba domin kaucewa kwari da cututtukan da kan kama amfani bayan a ciro shi.
d. Za a dinga goge fuskokin bangwayen da kofofi da taguna a ko wane mako.
e. Za a dinga tsaftace saman teburin wawwarewa da na karkasawa kana a sanya sinadarin magani a wanke a ko wane karshen zangon canjin aiki.
f. Za a tabbatar an goge daben guraren tattarawar masu sanyi gabani da yayin ajiya kana a sanya musu maganin kashe kwayoyin cututtuka bayan kwashe amfani kafin a loda wani amfanin da aka sarrafa.

#### Tsaftace wajen filin

a. Za a tabbatar da tsaftar wajen ginin. Itatuwa da tsinkaye da ciyayi a kone su.
b. Ba a bukatar dabbobi. Ba za a yi kiwon awaki ko shanu ko aladu ko kuma wasu dabbobin irinsu a muhallin guda ba.
c. Idan ana amfani da karnuka wajen gadi, dole ne a killace su lokutan aiki a wurin da ya dace.
d. Dole ne a ware wuri na musamman da ya dace domin rufaffun mazuban shara da mazubai da kuma ragowar abinci.

## KIWON LAFIYA DA KARIYA

### Agajin gaggawa

a. Dole a tanadi kayan kuma cikin sauki.
b. Dole ne a tanadi muhimman kayayyakin (maganin kashe kwayoyin cuta da bandeji da sinadarin rage radadi da kuma sinadarin kashe guba) da sinadarin gishiri mai saurin farfado da mutum da kuma sinadarin gyaran gabobi.

## KUDIN DA ZA A BUKATA

Kudin da ake bukata wajen gina gidan tattara amfani ya dogara ne ga yanayin tsarin da aka yi da kuma yawan kayan da za a dinga sarrafawa a ko wace rana. Sai dai kuma, za a iya samun misalin jarin da ake bukata na gidan tattara amfanin daga hukumar kamfanin GEMS4; kazalika kudin gudanawar gidan da kudin shigar da ake fatan samu sakamakon tafi da gidan ana lissafawa kuma a same su daga gare su. Ana iya samun jadawalin bayanan kudin da za a batar da wadanda za su shigo yayin gudanar da gidan tattara amfanin a nan gwargwadon bukata.

GEMS4
Mai sari/ mai kasawa

coffey
A TETRA TECH COMPANY

Office: St. James House 167 Cadastral Zone
Adetokumbo Crescent Wuse II, Abuja, Nigeria.
www.gems4nigeria.com +234 (0) 9290 1232
info@gems4nigeria.com